
# Akwai bege ...



## ga mutum kamar ni?

Wani dare, bayan taron falkaswa a wani babban guri, sai wani mutum wanda daga ganin shi yana da hatsari ya nufi maiwa'azin ya tambaye shi, "Ko za ka yarda ka zo tare da ni a daren yau? Domin ina so in yi magana da kai."

"Da farin ciki kuwa," mai wa'azin ya amsa.

Sai mutumin ya jagoranci tafiya a titunan anguwan har zuwa gidan sa. Sai ya bude kofa, ya ingiza mai wa'azin zuwa ciki daga nan sai ya fitar da bindiga. "Ba zan yi maka illa ba. Ina so ne in tambaye ka ko kana nufin abin da ka fada da gaske ne a wa'azin da kayi da daren nan ne, cewa jinin Yesu Kristi ya wanke mu daga dukan zunuban mu?"

Mai wa'azin ya amsa mishi cewa, "kwarai kuwa haka nike nufi. Allah ya fada a cikin maganan sa."

Sai mutumin ya ce, "Na kashe mutane hudu da wannan bindigan. Akwai bege ga mutum kamar ni?"

"Na sake gaya maka kuma, idan mutum zai furta ya kuma rabu da dukan zunuban shi Allah ya yi alkawari ya yafe shi ya kuma wanke shi daga dukan zunuban shi." (1Yahaya 1:7).

Sai mutumin ya ci gaba da cewa a gefe daya na wannan bangon akwai dandali na. Muna sayar da barasa ga kowa. A yawancin lokuta nikan karbi kudi na karshe daga mutum har ya rasa na sayen abinci ga iyalin sa. A gefen dandalin kuma gidan caca ne da sauran ayyuka na iblis. Har wani mutum ya taba yin kisan kai domin ya yi asaran komai a wurin. Akwai bege ga mutum kamar ni?"

Mai wa'azin ya amsa, da cewa "Allah yana nufin idan ya ce, 'JininYesu Kristi yana wanke mu daga dukan zunuban mu.'"

"Wani tambaya kuma bayan nan sai ka tafi. I dan ka bar wannan dandalin, za ka wuce gida na. Matana tana tare da diya ta mai shekara goma sha daya. Shekara goma sha uku da suka wuce, na sadu da wata yarinya mai kyau a New York, na yi mata karya akan rayuwa na. Sai ta aure ni amma bayan da ta tabbatar da gaskiyan, sai ya raunana mata zuciya. Tun daga wannan lokaci na sa ya zama mata "kiyama a duniya". Yanzu ma na fara dukan ta. A kwanan nan na mari diyata har na tura ta, ta fadi a murhu mai zafi, wanda ya kone ta daga kafada zuwa ga yatsun ta na hannu. Har hannun ya gurgunce na har abada. Akwai bege ga mutum kamar ni?"

Mai wa'azin ya kama wannan mutumin ya girgiza shi sosai, yace ka saurareni da kyau kaji. Duk wani irin abin da kayi a wannan duniya, maganar Allah tana tsaye "JininYesu Kristi yana wanke mu daga dukan zunuban mu." Wannan yana nufin kai/ke!"

Sai mutumin yace, "Na gode sosai. Na so in tabbatar ne. Na yarda da kai. Zan sake zuwa wurin taron ku gobe da daddare kuma."

Bayan da maiwa'azin ya tafi, sai mutumin ya fitar da dukan kayan cikin mashayarsa da kayan cacansa. Ya farface kwalban da gilas gilas. Ya kakarya teburan caca da kafafunsu. Ya kone su ludo da katin caca a cikin wuta. Dukan tsawon daren, ya lalatar da dukan kayan da sukan sa shi zunubi. Har sai da safiya sa'annan ya je ya zauna a kofan gidan a gajiye.

Daga jin shi ya dawo sai matan ta ce wa diyan "ta je ta ce mishi, Baba abincin safe yana shirye domin ka."

Diyar su ta tafi a hankali zuwa ga baban. Ta bi a tsorace, ta ce mishi "Baba, Mama ta ce abincin safe yayi."

Sai mutumin da murmushi ya ce, "kaunataccen 'yata, Baba baya bukatan abincin safe."

Diyar sa ta koma da gudu zuwa dakin girkin abinci ta ce "Mama! Baba ya yi mini murmushi ya kuma kirani kaunatacce na, bai yi mini ihuba!"

Maman ta ce; "ni ban yarda ba! Koma ki dai fada mishi abincin safe ya nuna." Sai maman ta bi ta a baya.

Da mutumin ya ji su suna zuwa sai mutumin ya yi murmushi ya ce, "Zo kusa."

Da rawan jiki, matan da diyan suka matso kusa da shi. A hankali ya sa hannayen shi ya rungumi su biyu din, da suka sha wuya a hannu shi, sai, da hawaye a cike a idanun sa sai ya tabbatar musu cewa; kada ku sake jin tsoro na kuma. Allah ya ba ku sabon Maigida da sabon Baba a yau."

A taro na wannan daren, matan da diyar su ma suka bada zuciyan su zuwa ga Kristi. Suma suka tabbatar da cewan "Jinin Yesu Kristi yana wanke mu daga dukan zunuban mu (1 Yahaya 1:7).

Ka sami sakon? Zaka furta ka kuma roki gafaran zunuban ka yanzu ka kuma bada ranka zuwa ga Kristi? Roki Allah ya yafe maka. Akwai bege domin wani kamar ka!

Hausa-7 "Is There Hope For A Man Like Me?"

Free tracts and biblical counsel available by request. Write:
**Word Of Truth,** P.O. Box 1126, Kaduna, Nigeria
Printed in USA